

Mallam Ilu yana zaune a kauyenmu kuma yana da kyanwa mai suna Safi.




Idan Malam Ilu ya
tafi aiki, yakan bar
ƙofa a buɗe.



Safi takan zauna a
bakin kofa tana
kula da gidan.



Idan karen
maƙwabtansu ya
matso kusa, safi
takan yi masa barazana.



Karen ya kan gudu.



Idan wani baƙo ya
ƙwanƙwasa ƙofa,
safi takan kai yakushi.




Baƙi sukan juya, su ruga a guje.




Idan Safi tana jin yunwa, ta kan rufe kofa.



Sai ta ci abincinta.



Daga nan Safi sai tayi tsalle ta haye doguwar kujera, ta yi barci har da minshari. Kurr! Kurr! Kur!



Idan Malam Ilu ya
dawo, safi sai ta
miƙe cikin farin ciki
tana yi masa maraba.



Malam Ilu da Safi
sukan zauna,
kowannensu yana
karanta jarida.